NATIONAL PENSION COMMISSION

*...Pension Guaranteed*

# Mafi Yawancin Tambayoyi

akan

# Tsarin Adashen Fansho

## Mafi  yawancin tambayoyi akan Tsarin Adashen Fansho

1. **Me ake nufi da Fansho?**

   Fansho (Pension) dai wasu kudade ne da ake biyan ma'aikacin da ya yi ritaya ko ya ajiye aiki, a kowane wata a sanadin tsawon shekaru yana aiki ko lalurar rashin lafiya, da nufin tallafawa rayuwarsa a lokacin da ya tsufa.

2. **Shi kuwa tsarin Adashen Fansho (Micro Pension Plan) yaya yake?**

   Wannan wani tsari ne na musamman a cikin tsarin fansho na kasa wanda ke bada dama ga ma'aikacin kashin-kansa wato wanda ba gwamnati ko wata hukuma yake yima aiki ba, ya rika tara kudade a hankali a hankali yadda zai karbi fanshonsa bayan ya daina aiki ko kuma a sanadin wata lalura.

3. **Don me mutum zai shiga wannan tsarin na Adashen Fansho (Micro Pension)?**

   Eh, tabbas tsari ne mai fa'ida da tanadin gobe tunda yake an ce 'AJIYA MAGANIN WATA RANA'. Lalle yana rage radadin talauci kuma ga shi da sauki tare da saukakewa.

4. **Anci nasarar wannan tsari na Adashen Fansho (Micro Pension) a wasu kasashe na duniya kuwa?**

   Sosai kuwa an samu gagarumar nasarar tsarin a wasu kasashe kamar Ghana, Kenya da kuma Indiya.

5. **Menene bambancin fanshon ma'aikatan gwamnati da wannan tsari na Adashen Fansho?**

   Eh haka ne fa, ai dukkansu suna bisa tsarin fansho na adashen gata da gwamnatin tarayya ta tsara a shekarar 2004. Bambancin kawai ya rataya ne cewar adashen gata na ma'aikacin gwamnati ne shi kuwa adashen Fansho na mai cin gishin kansa ne.
   Kaga dai shi tsarin fansho na ma'aikatan gwamnati TILAS ne ga duk wanda gwamnati ko wata hukumar gwamnati ko hukuma mai zaman kanta ta dauka aiki ya bada wani kaso daga albashinsa a kowane wata domin zubawa a cikin asusun sa na ajiyar fansho.
   Shi kuwa na Adashen fansho (Micro Pension Plan) na ganin dama ne kuma sai wanda ya shige shi zai rika zuba kudin da ya ga zai iya a cikin asusun sa na ajiyar fansho a kowane wata.

6. **To su wane ne ka iya shiga wannan tsari na Adashen Fansho?**

   Mutum na cancanta ya shiga wannan tsari idan ya cika wadannan sharudda.
   a) Ya kasance shi dan Najeriya ne kuma akalla ya kai

shekaru 18 da haihuwa.

b) Ya kasance ya na neman kudinsa ta hanyoyin da dokokin kasa suka yadda da su.

c) Ya kasance mutum na cikin wata kungiya ta masu sana'o'i ko aikin musamman

d) Ya kasance yana da wurin neman abinci ko kamfani ko masana'antar da ma'aikatanta basu kai mutane uku ba.

7. **Shin mutum na iya mallakar Asusun ajiyar fansho (Retirement Savings Account - RSA) fiye da daya kuwa?**

   A'a, doka bata yadda da mallakar Asusun kudin fansho (RSA) fiye da daya ga kowa ba.

8. **Ko ma'aikacin da ke cikin tsarin fansho na kasa, kuma yana da RSA zai iya shiga tsarin Adashen fansho?**

   A'a, doka bata yadda mutum ya shiga tsari guda biyu ba.

9. **To yaya ne zan shiga tsarin Adashen fansho (Micro Pension)?**

   Duk wanda ya cika sharuddan shiga wannan tsarin na

iya zuwa kai tsaye ga kamfanin fansho (Pension Fund Administrator - PFA) wanda yake so, ya cika takardar fom na rajista domin shigar da shi cikin tsarin. Idan anyi masa rajista za a bashi lamba ta musamman wadda da ita za'a rika amfani da wurin dukkan hulda tsakanin shi da kamfanin fanshon daya zaba.

**10. To a ina zan samu kamfanin fansho da nake so?**

lallai kuwa akwai jerin sunayen kamfanonin fansho (PFAs) idan ka bude shafin Hukumar Manhajar Fansho ta kasa a intanet da wannan adireshin na: www.pencom.gov.ng.

**11. Wanene ke da alhakin kula da kudaden Adashen fansho?**

Duk kamfanin da ka zaba, shi ke da hakkin kula da kudaden adashenka, sannan kuma kamfanin ajiyar kudin fansho (Pension Fund Custodian – PFC) ke da alhakin ajiyar kudin da cikakkiyar amana.

**12. Wadanne shirye-shirye Hukumar Manhajar Fansho ta kasa ta yi domin tabbatar da cikakken tsaro na kudin Adashen Fansho?**

Lalle akwai ingantaccen tsarin sa-ido wanda Hukumar Manhajar Fansho ta kasa ta tanada inda a kullum tana bin hada-hada da hannayen jarin da aka zuba wadannan kudi wanda kamfanonin fansho suke rike

da su domin tabbatar da cewa suna yin komi bisa ka'idojin sarrafa kudi da zuba jari wadanda gwamnati ta amince da su.

**13. Ko akwai wani tsari na kariya bisa kudin jarin da aka zuba cikin wannan tsari na Adashen fansho?**

Haka ne fa, kamfanin ajiyar kudin fansho (PFC) ya bada garanti da kariya ga duk kudaden dake cikin wannan tsari kuma zai dauki nauyin biyan duk asarar da aka yi ta hanyar batan kudin.

**14. Ta yaya ne ake iya samun riba ko karuwa akan kudin da aka zuba ta wannan tsari na Adashen Fansho?**

Eh haka yake, tunda dama can su kamfanonin fansho (PFAs) suna saka jari ne da kuma jujjuya wadannan kudin adashen fansho, dukkan irin ribar da aka ci ta hanyar kasuwancin da suka yi ana raba ta ne ga masu rajista da tsarin.

**15. Ko za a rika cire mani haraji daga kudin da na saka a wannan tsari na Adashen Fansho?**

A'a, ko da wai! Bisa dukkan tsare-tsaren da Hukumar Manhajar Fansho ta yi, ba a cire harajin ko kobo daga cikin kudin da aka zuba cikin asusun fansho ko ribar da kudaden suka jawo.

**16. Ko ina da zabin irin yadda ya kamata a sarrafa kudina wajen zuba jari?**

Anan ma dai, a'a. kamfanonin fansho ne ke da alhaki da zabin inda za su saka jari bisa sharuddan da Hukumar Manhajar Fansho ta Najeriya ta ayyana.

**17. To shin wai shi wannan tsari na Adashen fansho ya bambanta da yadda asusun ajiya na bankunan kasuwanci ke gudana?**

Kwarai kuwa. lalle tsarin Adashen Fansho ya sha bamban da asusun ajiya na bankunan kasuwanci domin duk kudaden dake cikin wannan tsari sai wata-wata ne kawai za'a iya dibarsu bayan mutum ya yi ritaya ko ajiye aikinsa, amma ka ga mutum na iya daukar kudin asusun ajiyarsa a duk lokacin da ya so, idan ajiyar a bankunan kasuwanci ne. Babban al'amari shine cewar shi Adashen Fansho, anayin sa ne domin mutum ya sami kudaden shiga bayan ya tsufa.

**18. Minene karancin kudin da zan rika zubawa a cikin tsarin Adashen Fansho ko wane wata?**

Babu iyaka ko karancin zubin da mutum zai iya yi a cikin wannan tsari na Adashen Fansho. Dai-dai ruwa dai-dai tsaki kuma zabi ya rage ga mutum. Idan ka zuba kudi masu yawa, to fanshonka zai yi kauri.

**19. To yaya ake yin zubin kudi a cikin Adashen Fansho?**

Mutum na iya zubi ko a kullum rana, ko a duk mako ko kuma duk wata-wata yadda duk ka zaba amma bisa sharuddan zubin ajiyar kudi kamar yadda dokar sarrafa kudi ta Najeriya ta tanada.

**20. Da wane salon zubin kudi zan yi amfani a cikin wannan tsari na Adashen Fansho?**

Lalle kana iya zubin kudi tsabar su, ko kayi taransfa, ta hanyar asusunka na banki zuwa na kamfanin fanshonka ko kuma ta duk wata hanya ko salon zuba kudi da babban bankin Najeriya ya tanada.

**21. Ko mai Adashen fansho na da damar yin jingina da asusunsa na Adashen Fansho domin ya nemi rance a wani wuri?**

Ko da wai! Doka bata yadda ayi amfani da kudin fansho ba a matsayin jingina domin amsar bashia wani wuri.

**22. Ko wanda ke bin wannan tsari na Adashen Fansho zai iya rancen wani abu daga ajiyarsa da nufin ya biya kudin bayan wani lokaci?**

Nan ma dai babu halin yin wannan rance domin kuwa Dokar Fansho ta shekarar 2014 bata bada damar yin

hakan ba.

**23. Yaya zan mori ko amfana da abin da na zuba a cikin wannan tsari na Adashen Fansho?**

Mutum na iya amfana ta hanyoyi biyu: na farko, ta hanyar gajerar kwasa. Watau zai iya dibar wani abu daga cikin asusun sa kafin yayi ritaya (ajiye aiki); na biyu kuma bayan ya bar aiki wato zai amshi fansho akan tsarin wata-wata.

**24. Ko mene ne gajerar kwasa?**

Wannan yana nufin mutumin da ke cikin wannan tsari na Adashen Fansho ya ce a bashi wani kaso daga cikin abin da ya ajiye, wanda ya hada harda ribar da ya samu, domin biyan wata bukatarsa ko magance wata matsalar kudi da ya fuskanta tun ma kafin ya kai lokacin ritaya ko ajiye aiki.

**25. To yaya ake karbar fansho a cikin wannan tsari?**

Wannan na nufin karbar kudin fansho a wata-wata wanda aka shimfida shi akan dukkan kudin dake cikin asusun fansho a lokacin da mai adashen fanshon ya bar aiki kamar yadda ka'idojin amsar kudin fanshon suka shinfida.

**26. Yaya zan yi gajerar kwasa?**

Mutumin da ya shiga wannan tsari na Adashen Fansho na da damar karbar wani kaso na kudin da ya tara ta hanyar rubuta neman yin hakan a rubuce ga kamfanin fanshonsa bisa ka'ida.

**27. Tsawon wane lokaci mutum zai dauka yana zubin kudi kafin ya nemi karbar wani abu daga cikin kudin da ya tara?**

Mai Adashen fansho na da 'yancin neman a bashi wasu kudi daga ajiyarsa bayan watanni uku da fara ajiya. Daga bisani zai iya daukar wani abu a kowane mako, daga abinda yayi saura daga cikin abinda aka iyakance na gajerar kwasa bayan.

**28. Wane lokaci ake dauka kafin samun kudin da mutum ya bukata daga ajiyarsa?**

Cikin kwana biyu kacal daga lokacin da aka nemi ayi kwasa a rubuce zuwa ga kamfanin fansho domin biyan abunda aka bukata.

**29. Me zai faru lokacin da mai Adashen Fansho wanda ya samu aikin gwamnati?**

Duk wanda ke Adashen Fansho sai kuma ya samu aikin hukuma, to kai tsaye sai ya rubuta wa kamfanin fanshonsa domin a shigar da shi a cikin tsarin fansho

na ma'aikatan hukuma. Haka zai ci gaba da yin amfani da asusunsa domin yin zubin fanshon ma'aikatan hukuma.

**30. Shekaru nawa ne dan Adashen Fansho ke ritaya?**

Wanda ke cikin wannan tsari na Adashen Fansho na ritaya ne idan ya kai shekaru hamsin (50) da haihuwa ko kuma a sanadin lalurar rashin lafiya. Sai dai kuma yana da zabin yaci gaba da yin zubi a cikin asusun shi ko bayan ya wuce shekara hamsin din. Watau ba sai ya bar aiki ba koda ya kai shekaru hamsin da haihuwa ko kuma ya wuce hakan.

**31. Bayan ritaya, ta yaya zan samu kudin da na ajiye na fansho?**

Dan Adashen fansho zai karbi fansho ta hanyar tsararren kason fansho a wata-wata (Programmed Withdrawal) ko kuma ta bin tsarin inshora da zai bada fanshon wata-wata har zuwa karshen rayuwarsa (Life Annuity).

**32. Yaya tsararren kason fansho (Programmed Withdrawal) yake?**

Wannan salo ne na karbar kudi gutsure-gutsure daga hannun kamfanin fansho da ka yi rajista da shi ko dai duk wata-wata ko kuma bayan watanni uku-uku.

**33. Shi fa tsarin fanshon Inshora na har karshen rayuwa (Life Annuity) yaya yake?**

Wannan salo ne na karbar kudin ajiyar dan Adashen Fansho ta hannun kamfanin Inshorar Kadara. Kuma tanadi ne mai tabbaci da zai ba da tabbacin samun fansho har iya rayuwa.

**34. Minene tsawon lokacin Tabbaci ko Kariyaa tsarin Inshorar Kadara?**

Lalle tabbacin mai Inshorar kadara ta 'Life Annuity' na kai tsawon shekara goma. Idan kuma mai Adashen Fansho ya fara amsar fansho bayan yayi ritaya to sai ya rasu kafin cika shekara 10 bayan ritayarsa, to za'a biya magadansa duk sauran hakkokinsa na fanshon da yayi saura har zuwa cikar shekaru goma. Idan kuma ya rasu ne bayan shekaru goma da ritayarsa to shi ke nan babu ko kobo da iyalansa zasu gada.

**35. Yaya za a yi da sauran kudin da ke cikin asusun dan Adashen Fansho idan ya mutu?**

Idan mutuwa ta faru, za'a biya sauran kudin ga magadansa kamar yadda ya bada a wasiyyar shi ko kuma kamar yadda yake rubuce a cikin takardar gudanar da gado daga Babbar Kotun Jihar da mamacin yake zaune ko kuma ta hannun wata kotu ko hukuma da ta umurchi kamfanin fanshonsa, a rubuce kai tsaye, cewar a biya magada kudaden dake

cikin asusun fansho na mamacin.

**36. Ko ina iya shiga tsarin Adashen Fansho bayan na yi ritaya daga aikin gwamnati?**

A'a, Babu halin yin haka. Doka ta bada dama ne kawai mai Adashen Fansho ya shiga fanshon Hukuma idan ya sami aikin gwamnati ko wata Hukuma mai zaman kanta.

NATIONAL PENSION COMMISSION
Plot 174, Adetokunbo Ademola Crescent Wuse II, P.M.B. 5170 Wuse, Abuja, Nigeria.
Email: info@pencom.gov.ng
www.pencom.gov.ng
Tel: +234 (9) 4603943, +234 902 979 7837